Ban taɓa ganin Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi yana ƙyaƙyata dariya ba, har inga ƙarshen ganɗarsa ba, kawai ya kasance yana murmushi

Daga Nana A'isha uwar muminai - Allah Ya yarda da ita - ta ce: Ban taɓa ganin Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi yana ƙyaƙyata dariya ba, har inga ƙarshen ganɗarsa ba, kawai ya kasance yana murmushi.
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Nana A'isha - Allah Ya yarda da ita - ta bada labarin cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - bai zama mai kai matuƙa a dariya ba har aga ganɗarsa ta sama ba, ita ce naman dake rataye a saman maƙogwaro, kawai ya kasance yana murmushi ne.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/3060